# FASAHAR BAHAUSHE TA FUSKAR NOMA, SASSAKA, JIMA, KIRA, DUKANCI DA MAKAMANTAN SU

Abubakar Ɗan Hassan Sanyinna, Abubakar Ɗanillela and Sani Ibrahim Sanyinnawal
Kwalejin Ilimi Ta Shehu Shagari
abubakarsardauna64@gmail.com

*TSAKURE*
*Manufar wannan mukala ita ce fitowa da wasu sana'o'in Hausawa na gargajiya da rabe-raben su da kayan aikin gudanar da su. Haka kuma mukalar ta dubi amfanin sana'a ga al'umma, da kuma yadda sauye-sauyen zamanin ke tasiri wajen habakar da sana'o'i ga al'umma.*

## GABATARWA

A wannan takardar zamu dubi fasahar Bahaushe ta fuskar yadda yake aiwatar da sana'o'insa na gargajiya. Sana'o'in da zamu duba sun hada da noma, kira, kadi, saka, rini, jima, sassaka, ƙuli-ƙuli, wanzanci, fawa, da kuma igidi. Kowace sana'a zamu dubi irin muhimman kayayakin da ake amfani da su wajen aiwatar da ita. Haka kuma za mu yi tsokaci a kan amfanin sana'a ga al'umma.

A ƙasar Hausa galibi maza ne ke yin noma, suna kuma haɗa noma da wata sana'a. Mafi yawa sun fi gwama noma da kiwo. Noma da sana'a su ne ginshiƙin rayuwa da kuma tattalin arzikin yau da kullum na Hausawa. Sana'a na ɗaya daga cikin muhimman manyan hanyoyin gane martabar mutum da kuma ƙasaitarsa da matsayinsa a cikin al'umma.

Kasancewar al'umma a duniya na da wasu muhimman hanyoyi da suke bi ko amfani da su wajen gudanar da harkokin rayuwarsu ta yau da kullum. Waɗannan hanyoyi suna ƙunshe da wasu muhimman fasahohi da aka gada kaka da kakanni, su ne suke taimako wa rayuwa wajen dogaro da kai da abin da ake ci a kuma biya buƙatun rayuwa.

Al'ummar Hausawa na kiran waɗannan hanoyoyi da sunan sana'o'i.

## ME AKE NUFI DA SANA'A?

Masana da yawa sun bayyana ra'ayoyinsu a kan abin da ake nufi da sana'a a Bahaushiyar al'ada. Misali:

A ra'ayin Yahaya, (2001: 84) cewa ya yi:

> "Sana'a hanya ce ta amfani da azanci da hikima, a sarrafa albarkatu da ni'imomin da dan Adam ya mallaka don buƙatun yau da kuma"

"Sana'a ita ce tushen rayuwar al'umma gaba ɗaya, wadda suke dogaro da ita don gudanar da tsarin rayuwa ta yau da kullum".

Shi kuma Sharifai (1990:) ya danganta sana'a da cewa:

> "Duk wata hanya da mutum yake bi don nema ko samun abinci, abinci yana zuwa ta hanyar kuɗi ko wani abin da rayuwa zatta dogara a kai. Kuma wannan hanya ta zama wadda aka gada ce tun iyaye da kakanni, ba wata baƙuwar al'umma ce ta kawo ta."


cc

Rabi'u (2002) cewa ya yi:

> "Duk wani aiki da za a yi don gudanar da wani abu da za a musaya a tsakanin wani da wani don samun abin masarufi".

Ra'ayina:

Sana'a hanya ce ta ba ni gishiri in ba ka manja da kuma hanyar mayar da taro sisi cikin hikima, azanci, da basirar da Allah ya albarkaci bil-adama da ita, wadda ake gudanarwa tsakanin jinsin bil-Adam da ke raye a doron ƙasa.

Wushishi (2011:26) cewa ya yi:

> "Sana'a wata hanya ce ta samun aiki, na dogara da kai don tanadar abubuwan biyan buƙatu da neman rufin asirin kan harkokin rayuwa da kuma sarrafa albarkatu ta hanyar kimiyya da fasaha da karkatar da su wajen saye da sayarwa da musayar koya don mallakar abin da za a iya samarwa kai".

Don haka idan muka yi amfani da kaifin hankalinmu da kuma la'akari da ra'ayoyin masana dangane da ma'anar sana'a, zamu iya cewa sana'a ita ce duk wata hanya da dan Adam ke iya sarrafa basirar da Allah ya hore masa cikin hikima don samar wa kai abin biyan buƙatun rayuwar yau da kullum. Sana'a ita hikima da basirar da dan Adam ke sarrafa albarka da Allah ya ba shi don samar da hanyar dogaro da rayuwarsa ta hau da kullum. Haka kuma dabaru ne na mayar da taro sisi cikin hikima don samun abin dogaro da kai.

## MA'ANAR FASAHA

Fasaha: A cewa kamusun Hausa Fasaha na nufin kwarewa ko gwaninta. Haka ma a wajen sana'a fasaha tana nufin a yi amfani da fasaha domin a sarrafa wasu albarkatun ƙasa don a samar da wasu ababen amfani ko more rayuwa.

A wannan muƙalar mun dubi fasahar Bahaushe a cikin sana'o'insa na gargajiya ta fannin kayan aikin da yake amfani da su domin cimma muradunsa. Misali sana'ar Noma, sana'a ce da take buƙatar kayan aiki a matakai daban-daban kamin a cimma amfanin sana'ar, kuma Allah ya baiwa Bahaushe fasahar gano waɗannan kayan aikin da za su taimaka masa ga cimma manufarsa.

## TAKAITACCEN TARIHIN SAMUWAR SANA'O'IN GARGAJIYA NA HAUSAWA

Tarihi ya nuna cewa, tun zamanin 'ya'yan Annabi Adamu wato ƙabila da Habila sana'ar ta faru wanzuwa a doron ƙasa. Ta hanyar sarrafa itace a matsayin garma da ake noma da ita. Ashe ke nan, samuwar sana'a wani daɗaɗen tarihi da ya fara wanzuwa tun farko halittar bil-Adama.

Tabbacin tarihin samuwar sana'o'in gargajiya na Hausawa abu ne mai wuya ga al'ummar Hausawa. Amma akwai hasashen ke cewa sana'a ta ɗan Adam akwai dalilan da suka samar da ita.

Tun kafin wannan nazarin akwai fahimtar cewa buƙatoci daban-daban na dan Adam su ne suka haifar da samuwar sana'o'i daban-daban na dan Adam saboda samun sauƙi tafiyar da rayuwarsa ta yau da kullum.

Daga cikin buƙatun dan Adam akwai "abinci" buƙatar abinci, ita ce ta haifar da sana'ar "noma". Domin babu wata rayuwa da ke inganta, ba tare da abinci ba. Saboda haka, idan za a samar da abinci, sai an nemi kayan aiki yin noma. Wannan hanya ce ta samar da kayan aikin noma ta haifar da sana'ar "ƙira".

Ire-iren wadannan buƙatu ne suka haifar da samuwar wasu daga cikin ƙananan da manyan sana'o'in gargajiya na Hausawa.

Alal misali, buƙatar sutura ce ta haifar da sana'ar "Saƙa". haka ma buƙatar ingantaccen muhali, ya haifar da sana'ar "gini". Haka dai abin ya cigaba da wanzuwa har zuwa lokacin da tunanin Hausawa ya faɗaɗa, buƙatun su suka ƙaru. Saboda haka sai sana'o'i suka ƙaru har suka samar da cikakkun abubuwan gudanar da rayuwar al'ummar Hausawa ta yau da kullum. Akwai hasashe cewa ta haka ne sana'o'in gargajiya suka ɓunƙasa kuma kowace zuriya ta kama sana'ar da ta fi dacewa da ita.

Har wa yau hasashe ya nuna cewa sana'o'in gargajiya sun taimaka wajen kafuwa da bunƙasar unguwanni da ƙauyukka da biranen ƙasar Hausa. Don fahimtar haka, ana iya kallon wasu unguwanni a manyan garuruwan ƙasar Hausa. Misali.

- Unguwar maƙerar Assada Sakkwato
- Majema unguwar Rogo Sakkwato
- Marina, 'yan marina, Sakkwato
- Unguwar 'yan gurasa, Kano
- Marnan gangu, Sakkwato,
- Madaka Sakkwato
- Maɗaunƙa, Sakkwato

- Unguwar 'Yan Awaki- Kano
- Unguwar Sakkarawa- Sanyinna
- Unguwar Wanzamai- Sanyinna
- Unguwar 'yan kifi- Kano
- Kasuwar 'yan Gwari- Kano
- Unguwar 'yan Taba-Katsina

## SANA'O'IN GARGAJIYA A JINSANCE

### (A) Sana'o'in maza

Waɗannan su ne yawanci maza ne suka fi yin su amma akan samu mata na yin su amma ba kodayaushe ba. Waɗannan sana'o'i su ne kamar:

Kira, koli, farauta, jima, wanzanci, gini, dako, su, noma, dukanci, sassaƙa, fatauci, faskare da sauransu.

### (B) Sana'o'in Mata

Waɗannan su ne ga al'ada mata ne kawai ke yin su, kamar: Kitso, kaɗi, ƙosai, sussuka, daɓe, daddawa, suya, tuwo da miya amma akan samu daidaikun maza masu yin wasu daga cikinsu a wasu lokutta.

(C) <u>Sana'o'in Tarayya</u>

Waɗannan sana'o'i ne da jinsin maza da mata ke yi, kamar: Noma, saƙa, ɗinki, arkoni, (awo), ginin tukwane, dillanci da sauransu.

## IRE-IREN SANA'O'IN GARGAJIYA NA HAUSAWA

### 1) NOMA

Na duke, tsohon ciniki wani bakandaman kirari da Hausawa ke yi wa noma.

"Noma dai shi ne tonon ƙasa da manoma kan yi da nufin renon shukkokin tsiro da suka shukka da nufin neman abinci da abin masarufi da rayuwa zata yi dogaro da shi". Garba (1997), da Maidabo (1979, da Dano 2004).

## NAU'IN KAYAN AIKIN NOMA NA GARGAJIYA NA HAUSAWA

Noma yana da kayayyaki da yawa da ake amfani da su wajen aiwatar da shi su ne:-

a. <u>Sungumi</u>: Sungumi wani nau'in kayan aiki gona ne mai doguwar ƙota da ƙarfe irin na fartanya, ana amfani da shi wajen sara ƙasa ko tona ƙasa, waton ramin da za a zuba iri.

b. <u>Manjagara</u>: Wannan nau'in kayan aikin gona, yana ɗauke da yatsun ƙarfe, ana amfani da shi wajen share dattin da gonar take da shi.

c. <u>Gatari</u>: Ana amfani da wannan nau'in kayan aikin gona n\e wajen sare rassan bishiya (itace) da suka kare sararin rana don samar wa shuka hasken rana kuma a kan yi amfnai da adda idan babu gatari.

d. <u>Fatanya/kalme</u>: Ana amfani da fatanya ko kalme wajen noma hakukuwa da suka fito cikin gona.

e. <u>Galma/garma</u>: Ana amfani da galma ko garma ne wajen jan kuyyan gona.

f. <u>Magirbi/Kwasa</u>: Ana amfani da magirbi ko kwasa don yin sassabe da girbe amfani gona.

g. <u>Lauje</u>: Ana amfani da lauje ne wajen yankan amfarin gona da ciyawa.

h. <u>Iggiya</u>: Ana amfani da iggiya ne don ɗaure amfanin gona domin samun sauƙin ɗauka. Har kirari a kan yi wa mutane a ce "Iggiya madaura kaya".

i. <u>Rumbu</u>: Rumbu shi ne wajen a dana amfani gona. A ƙauyukan Sakkwato akan kira rumbu da sunan Rutawa (da ake amfani da su wajen aiwatar da noma).

## IRE-IREN NOMA

Bahaushe yana da yanayin shekara iri biyu Akwai yanayin damana da kuma yanayin rani amma kuma akwai bazara da hunturu.

a. <u>Noman Damina</u>: Wannan nau'in noma ne wanda ake yi a lokacin damina, lokacin ruwa sama Abubuwan da ake nomawa a wannan lokaci sun haɗa da: Gero, dawa, gyaɗa wake, masara, rogo, dankali da sauransu.

b. <u>Noman Rani</u>: wannan nau'in noma ana gudanar da shi ne lokacin rani, waton lokacin da ruwan damina suka ɗauke. Ana gudanar da wannan nau'in noma ne a fadama da gulaben da ba su ƙafewa. Ana noma kayayyaki neman kuɗi da kayan maramari.

<u>Ana noma kamar</u>: Albasa, dankali, rake, tumatir, tarugu, shinkafa, karas, tattasai da dai sauransu.

## 2) KIRA

Wata sana'a ce da ake amfani da tama da karfe ta hanyar narke su da wuta ta hanyar zuga-zugi a zaurukan ƙira na gargajiya.

Masana sun ba da ma'anar ƙira kamar haka:

> Bello (2006) cewa ya yi:
> "Narka ƙarfe da sarrafa shi domin samar da ma'aikaci kamar fatanya ko galma".
>
> Sharifai (1990) cewa ya yi:
>
> "Kira ita ce narke ƙarfe ko tama ko sanholanna ko azurfa ko zinari da wuta, a mayar da ita wani abin amfani, ƙira sana'a ce ta gargajiya da ta shafi sarrafa ƙarfe don samar da waɗandu abubuwan buƙata ko amfani ga jama'a.

Don haka ƙira ana iya cewa sana'a ce da ake sarrafa ƙarfe da madangantansa don samar da wasu abubuwa na ƙawa da amfani a sauran ɓangarorin rayuwar yau da kullum. Haka ma ƙira sana'a ce da ake sarrafa nau'o'in karfe da al'umma ke dogaro da su ta fuskoki daban-daban tun ma ba noma ba.

## NAU'O'IN KAYAN AIKIN KIRA

a. **Karfe**: Wannan shi ne ginshiƙin gudanar da sana'ar ƙira saboda da shi ne ake sarrafa kayan da ake samarwa don sauran sana'o'in gargajiya
b. **Sanholama:** Wannan wani nau'in ƙarfe ne da ake sarrafa shi don samar da wasu abubuwa kamar su lukwanan ƙarfe, kuyafu da cukulla.
c. **Azurfa**: Wannan wani nau'in ƙarfe da aka sarrafawa don yin kayan kwalliya na mata da sauran kayan kyalkyalin daki.
d. **Zinari**: Wannan ƙarfe ne da ya fi sauran nau'o'in ƙarfe daraja da ɗaukaka. Ana sarrafa zinari a yi kayan kwalliyan mata kamar sarka, zobe da 'yan kunne da sauransu.
e. **Wuta**: Wuta muhimmiya ce wajen kayan aiwatar da sana'ar ƙira. Da wuta ne ake narke sinadaran da ake amfani da su wajen ƙira.
f. Uwar-Maƙera: Uwar maƙera ita ce ƙarfen da ake kafawa a ƙasa don ɗora ƙarfen da aka gasa da wuta don a sarrafa shi, a maida shi wani abu.
g. Zuga-Zugi: Zugazu-zugi, fatar akuya ce da aka jeme, aka fitar da ƙofofi biyu don fura wuta.
h. Awartaki:Wannan wani ƙarfe ne da aka tanada, don tsame gasasshen ƙarfen da aka saka shi a wuta don sarrafawa. Maƙera na amfani da awartaki ne don riƙe ƙarfe mai zafi. Har Sani Aliyu Dandawo na cewa: "Yara ka sa awartaki ga wuta don saboda zafi". Waƙa S/Maƙera".
i. **Masaba:** Masaba wani mulmullallen ƙarfe ne da ake amfani da shi wajen sarrafar da ƙarfen da aka narka ko gasa don samar da wani muhimmin abu.
j. **Kurfi:** Wani ƙarfe ne da ake amfani da shi wajen datsa ƙarfe. Ana amfani da masaba wajen sarrafa kurfi don datse ƙarfe.

k. Mahuji: Wani ƙarfe ne mai tsini da ake amfani da shi wajen huda ɓotar ma'aikaci kamar kwasa ko fatanya da sauransu.
l. Zarto: Ana amfani da zarto ne wajen wasu abin da ake son ya yi kaifi kamar wuƙa, mashi, takobi, adda da sauransu.
m. Gawayi: Wannan muhimmin ne wajen gudanar da sana'ar ƙira, maƙera na amfani da gawayin ƙirya don ya fi jure cin wuta. A taƙaice dai duk waɗannan da aka ambata a sama ta hanya rkir ane ake samar da su.

IRE-IREN KIRA
Kira ta kasu gida biyu, akwai ƙirar baƙin ƙarfe da ƙirar farin ƙarfe.
a. Kirar baƙin ƙarfe: wannan nau'in ƙira ne na amfani da ƙarfe mai nauyi don yin abubuwa kamar hauya, lauje, kwasa, galma, baho, da sauransu.
b. Kirar farin ƙarfe: Wannan nau'in ƙira ce ta amfani da ƙarfe maras nauyi kuma mai sauƙi narkewa don yin abubuwa kamar tuƙunya ƙarfe, ludayin ƙarfe, zobe, sarka da sauransu.

3) WAZANCI
Wannan sana'a ce da ake danganta ta ga wani aiki da ake gudanarwa da ya shafi al'adun Hausawa. Masana sun tofa albarkacin bakinsu a kan ma'anarta. Daga cikinsu akwai:

Bello (2006) ya ce:

> "Sana'ar yin aski da kaciya da sauran su ce".

Garba 1991:107, ya ce:

> "Wanzanci, sana'a ce ko kuma al'ada ce ta Hausawa da ake amfani da aska domin aske gashin kai da yanke loba".

Alhassan da Musa da Zaruruk (1982:65) cewa suka yi:

> "Wanzanci sana'a ce ta yin amfani da aska don aske gashi da yanke loba da yin tsaga ko ƙaho saboda rage ƙazanta da neman lafiya da tsare tafiya".

Don haka wanzanci na nufin amfani da aska don kauda ƙazantar da ta shafi gashin kai da na jiki da yin kaciya da tsaga don al'ada da neman lafiya kamar kaho da sauransu. Haka wamzamai su ne ke gyaran targaɗa ko kariya a al'adance.

KAYAN AIKIN WANZANCI
Daga cikin kayan aikin wanzanci akwai:
a. Aska: Aska kusan ita ce jigon gudanar da sana'ar wanzanci, saboda ita ce wanzanmai ke tinƙaho da ita wajen gudanar da sana'arsu ta wanzanci, musamman wajen aski da sauransu.

b. **Kaho:** Kaho ana samun sa daga ƙahonin sa ko saniya. Yin ƙaho hanya ce ta samar da lafiya ga jama'a. Daga ƙarshensa sai a yanke tsinin don a sami kofar da za a riƙa tsotso jinin maras lafiya.

c. **Dogari**: Dogari wani itace ne da ake amfani da shi a lokacin da wanzami ke ƙoƙarin cire wa mutum belu (hakin wuya). Amfaninsa don danne doron harshe don a sami hango belu da za a cire.

d. **Koshiya**: Koshiya shi ne ƙarfen da ake amfani da shi wajen cire belu ga mutum.

e. **Tanƙolo**: Tanƙolo, wata fata ce da wanzammai ke amfani da ita wajen wasa asksarsu ta aski. Dukawa ne ke samar wa manzanmai wannan fata. Jemamma ce ana rina ta da jar garura.

f. **Dutse**: Wannan ma abin wasa aska ne ta wanzanmai. Wano lokaci sun fi son amfani da dutse maimaikon tanƙolo. Wasu kan kira wannan dutse kankara.

g. **Tasa ko kofi**: Wanzanmai na amfani da tasa ko kofi wajen zuba ruwa a lokacin da suke yi wa mutane aski.

h. **Ruwa da sabulu**: Ruwa da sabulu wasu abubuwa ne da wanzanmai ke amfani da su wajen yin sana'arsu ta wanzanci. Suna amfani da ruwa wajen shafa wa mutum sabulu.

i. **Kara**: Wanzanmai na amfani da kara a wurare da yawa. Suna amfani da kara a lokacin da suka yi wa yaro kaciya don tallabe kaciyar don kada ta shafi jikin yaro. Haka ma suna amfani da kara wajen yi wa yaro karkiya ko marri don ta hana yaro haɗe ƙafafunsa a lokacin da yake yin barci ko kwana. A kan yi amfnai da kara idan an ɗora hannu ko kafar da ta karye.

j. **Hantsaƙi**: Hantsaƙi wani ƙarfe ne da wanzanmai ke amfani da shi wajen cire wani abu da ya maƙale wa mutum kamar ƙaya ko wani abu da ya shige wa wani a cikin kunne. Hantsaƙi yana da tsini da kuma baki biyu a wurin mariƙansa.

k. **Zabira**: Zabira ita ce jakar da wanzanmai suke zuba kayan gudanar da aikinsu ta wanzanci. Duk abubuwan da suke amfani da su na cikin zabirar in ban da tasa da tanƙolo.

l. **Magani**: Wanzanmai na bada magungunan cututtuka da yawa. Akwai maganin na sha da na barbaɗawa da shafawa.

## 4) SASSAKA

Sassaƙa sana'a ce da masu aiwatar da ita suke da muhimmanci ga rayuwar Hausawa.

Masana sun bayyana ma'anar sassaƙa kamar haka. Alhassan da Musa da Zarruƙ (1982:54) sun ce:

> "Sassaƙa na nufin sarar itace da sassaƙa shi ta sifofi daban-daban da nufin jarrata shi zuwa dukkan abubuwan da ake bukata".

> Bello (ed) (2006:393) cewa ya yi:
> "Sana'ar sassaƙa sana'a ce ta sarrafa itace don samar da surori abin da aka sarrafa daga itace kamar allo da turmi da mutum-mutum".

## KAYAN AIKIN SASSAKA

Sana'ar sassaƙa tana da wasu muhimman kayan aiki kamar haka:

a) **Itace**: Itace su ne ƙashin bayan sana'ar sassaƙa don su ake sarrafawa don samar da duk wani abu da ake buƙatar sassaƙawa. Itacen da masassaƙa ke sarrafawa sun haɗa da: Gawo, ƙirya, kaɗanya, marke, da kuma dogon yaro.
b) **Gatari**: Gatari shi ne abin da ake amfani da shi don sare itacen da ake buƙatar sarrafawa.
c) **Gizago**: Gizago wani abin aiki ne da masassaƙa ke amfnai da shi wajen fitar da cikakkiyar surar abun da ake son samarwa.
d) **Mahuri**: Wani abu ne da ake amfnai da shi don fitar da ƙofa ko rame a jikin itacen da ake son sarrafawa don samar da turmi ko kujera da sauransu.
e) **Igiya**: Igiya ita ake ɗaure itacen da ake sarewa don kada ya faɗa wurin da ba a son ya faɗa. Haka da ita ake ɗauro kayan da aka sassaƙa a daji.

## 5) JIMA

Jima wata irin sana'a ce mai wahala, saboda tana ƙunshe da ƙyama. Yawancin wurin da ake yin ta, wuri ne mai tsananin wari da ƙazanta, har akan toshe hanci idan an bi ta wurin.

Masana sun bada ma'anar jima kamar haka:

Bello (2006) ya ce:

> "Jima ita ce fitar da gashi daga jikin fatar dabba don a sarrafa ta."

Haka ma Alhassan da Musa da Zarruƙ (1982:56) sun ce:

> "Jima sana'a ce ta sulluɓe fata da fitar da gashin da ke jikinta."

Garba (1991:31) cewa ya yi:

> "Jima ita ce sana'ar sulluɓe fata da fatar da gashin na asali ta hanyar amfani da bagaruwa da toka da majema da awartaki da kwatarniya da dutse da gungume da gwafa da igiya."

Don haka sana'ar jima sana'a ce da ake cire gashin da yake a jikin fata da nufin sulluɓe ta, ta hanyar amfani da wasu muhimman abubuwa.

## KAYAN AIKIN JIMA

Sana'ar jima, sana'a ce da ke buƙatar wasu kayayyaki, su ne kamar:

a) **Fata**: Fata ita ce ginshiƙin gudanar da sana'ar. Fata ce ake jemewa don a samar wa sana'ar dukanci kayan sarrafa.
b) **Kwatarniya**: A cikin kwatarniya ce ake haɗa dukkan abubuwan da ake tanada don jema fata. A cikin ta ne ake jiƙa sauran kayan haɗi na jima.
c) **Sanda**: Sanda, icce ce da majema ke amfani da ita wajen motsa jikon da aka yi na abubuwan da aka jika. Da sanda ne ake amfnai don a jawo fata daga cikin kwatarniya.
d) **Bagaruwa**: Bagaruwa ce ta farko da ake tanada don samun nasarar cire gashi don ba fatar launin da ake so.
e) **Toka**: Tokar da aka ƙone itace da ita ake haɗa kayan jima. Ana zuba ta ne kai tsaye, ba tare da an tace ta ba.

f) <u>Fatakko</u>: Wannan wata ciyawa ce da ake amfani da ita wajen haɗa kayan jima don taimakawa wajen samun sauƙin sulluɓe gashin jikin fata don ta yi santsi.
g) <u>Turmi ko Gungume</u>: Ana amfani da turmi ko gungume wajen shimfiɗa fata a lokacin da ake aiwatar da jima. Amfanin turmi ko gungume saboda a jikinsu ne ake shimfiɗa fata don a darje ta da dutse, a cire gashin ta.
h) <u>Dutse</u>: Da dutse ne ake darje fata a lokacin da ake son ganin an cire gashin da yake a jikinta.
i) <u>Turi</u>: Da turi ne ake samar wa fata da launin da ake son fatar ta kasance da shi. Ana amfnai da shi ne don inganta kyan fata bayan an jeme ta.
j) <u>Gwafa</u>: Gwafa dai ice ce mai harshe biyu, ana sarkafa fata a jikinta don a tsaftace ta da kuma cire mata duk abin da zai ɓata ta.
k) <u>Igiya</u>: Ana amfani da igiya don shanya jemammar fata.

## 6) DUKANCI

Sana'ar dukanci, sana'a ce kamar sauran sana'o'in gargajiya na Hausawa. Masana sun bayyana ra'ayoyinsu game da ma'anar dukanci. Wasu masana na ganin cewa, sana'ar dukanci, sana'a ce da ake sarrafa fata don samar da wasu muhimman kaya na amfanin yau da kullun na Hausawa. Alal misali kamar: Takalman fata, jaka, sirdin dawakai, kuben takubba, da na wuƙa da sauransu.

> "Dukanci sana'a ce da ake amfani da fatun dabbobi kamar shanu da damisa da rakumi da tumaki da barewa da gada. Haka ma ana amfani da fatun ƙwari kamar irin su maciji da kada da damo. Akan sarrafa fatun wasu manyan tsuntsaye kamar irin su Jimina, da ɗawisu don yin mafitai da wasu kayan ƙawa da ake ƙawata jikin ginin fadar sarki ko attajirai".

Dukawa sun kasu kashi biyu. Akwai masu yawon neman aikin gyaran kayan fatu, akwai na zaune wuri guda.

## KAYAN AIKIN DUKANCI

Kayan aikin dukanci sun haɗa da:

a) <u>Fata</u>: Fata ita ce ginshiƙin sana'ar dukanci, domin fata ce ake sarrafawa wajen samar da kayayyakin sana'ar dukanci ke samarwa.
b) <u>Wuƙa da Almakashi</u>: Wuƙa da almakashi wasu abubuwa ne da dukawa ke yanka fatu a lokacin da suke aiwatar ko amfani da su don sana'arsu ta dukanci.
c) <u>Kulƙi</u>: Kulki wani ice ne da dukawa ke amfani da shi wajen bubbuga fata don ta yi yadda suke buƙata a lokacin da suke son sarrafa ta, don aiwatar da wani abin bukata na rayuwar jama'a.
d) <u>Tsinke</u>: Tsinke shi ne ƙarfen da dukawa ke amfani da shi wajen ɗunkin fata don samar da abubuwa da sana'ar dukanci ke samarwa.
e) <u>Allura da Zare</u>: Allura da zare da su ne dukawa ke amfani wajen ɗinke duk wani abu da suka sarrafa fata don samar da shi. A jikin allura ne ake saƙala zare don samun sauƙin gudanar da ɗinki.

f) **Tuwo da Ɓula**: Ana amfani da tuwo ko ɓula wajen manne fata ko fata da wani abu da ake son haɗa shi da shi da fata don sarrafa su a samar da wani abin moriyar ga rayuwar Hausawa.

## 7) KAƊI

Kaɗi sana'a ce daɗɗɗiya a ƙasar Hausa. Haka ta hanyarta ce ake samar da zaren da masaƙa ke amfani da shi wajen aiwatar da sana'arsu ta saƙa.

Masana da yawa sun gudanar da bincike a kan sana'ar kaɗi a ƙasar Hausa. Sun bada ma'anar sana'ar kaɗi kamar haka:

Garba (1991) ya ce:

> "Kaɗi shi ne sarrafa auduga don samar da zaren da masaƙa ke saƙa sawaye da shi don samar da sutura".

Bello (ed) (2006) cewa ya yi:

> "Kaɗi shi ne yin zare ta hanyar gara mazari tare da auduga da ke dumbuzai a sillen kara".

Don haka ana iya cewa kaɗi, shi ne sarrafa auduga ta hanyar amfani da mazari da alli da taskira ta hanyar gara mazari don samar da zare da ake amfani da shi wajen aiwatar da saƙa.

Ana sarrafa auduga ne ta hanyar tsaftace ta tare da cire mata gulalan da ke cikinta da karkaɗe mata duk wani datti da yake maƙalle a jikinta. Sa'annan a warware ta, sai a karkaɗa ta da kara don ta yi laushi wajen kada ta.

## KAYAN AIKIN KAƊI

Kaɗi yana da wasu muhimman kaya waɗanda ake amfani da su don gudanar da sana'ar ta kaɗi. su ne:

a) **Auduga**: Auduga kusan ita ce babbar muhimmiyar abu wajen sana'ar kaɗi. Saboda ita ce ake amfani don aiwatar da duk wani abu da ya shafi kaɗi. sauran abubuwa 'yan rakiya ne ga auduga.

b) **Mazari**: Mazari nada muhimmanci kwarai da gaske wajen aiwatar da sana'ar kaɗi, domin in babu shi, ba a samar da zare. Akwai mazari guda biyu, akwai mazari na tariya da kuma mazari na kaɗi.

c) **Alli**: Alli wani abu ne da ake samar da shi daga ƙashi. A wasu wurare ana samun alli ne daga haƙowa da ake yi daga ƙasa. Wannan alli ana kiransa KARMATAKO. Amfani alli, shi ne taimakawa ga mai kaɗi ta sa hannunta ya yi santsi a lokacin da take murza mazarin da take kaɗi da shi.

d) **Lefe**: Lefe dai wuri ne da aka tanada don adana auduga bayan an tsaftace ta daga datti. Lefe ma'adani ne na auduga don kare ta.

e) **Kara**: Masu sana'ar kaɗi na amfani da kara ne wajen tara auduga a jikinsa don samun sauƙin gudanar da kaɗi. Masu kaɗi kan yi amfani da kara wajen bubbuga auduga a lokacin da suke son ko ƙoƙarin tace auduga, daga datti ko warware ta daga dunƙulewar da take yi bayan an cire mata gulalan da ke cikinta.

f) <u>Mataki</u>: mataki shi ne shimfiɗar da ake gara mazari ta kanta. Ana amfani da shi ne don samun sauƙin gargarawar mazari a lokacin da makaɗiya take gara shi.
g) <u>Taskira</u>: Taskira da ita ce abin da ake shirya kayan kaɗi a cikinta. Ana amfani da kwadon auduga wajen yin taskira. 'Yar kwacciya ce (KoKo) mai faɗI kamar maras zurfi ta hanyar shimfiɗa mataki a cikin ta, yadda za a iya gara mazari cikin sauƙi. masu kaɗi kan yi ajiya a cikinta musamman ajiyar kuɗi.

## 8) SAƘA

Saƙa sana'a ce ta gargajiya wadda take jingine da sana'ar kaɗi. Masaƙa kan saƙa sutura ta amfani da zare don samar da kowane irin tufafi na Hausawa. Akwai zare iri biyu da masu kaɗi ke samarwa, akwai zaren ABAWA da zaren ƁARTAKE, masaƙa na amfani da zaren abawa wajen saƙa sutura. Amma zaren ɓartake ana amfani da shi ne don yin wasu abubuwa kamar naɗe laya.

## KAYAN AIKIN SAKA

Wannan sana'ar ta saƙa na buƙatar waɗannan abubuwa su ne:

a) <u>**Masaƙa:**</u> Masaƙa wuri ne na gudanar da sana'ar saƙa. akwai wurare har guda uku masu muhimmanci ga masaƙi. Da farko akwai kusuwar daki. Wannan wuri ne da masaƙa mata kan yi amfani da shi a cikin ɗakunansu. Akwai kasuwar a zure, wannan maza ne tsofaffi ke amfani da shi. Sai kuma wani wuri kamar gindin wata babbar itaciya (bishiya) inda masaƙa ke kafa masaƙarsa don gudanar da saƙa.
b) <u>Itacen Gwafa</u>: Itacen gwafa, icce ne da ake amfani da shi wurin masaƙa. Icce ne da yake ɗauke da rassa biyu. Masaƙa na kiransa Turaku. Ana haƙa rami sai a kafa shi don a samar da ginshiƙin masaƙar.
c) <u>Igiya</u>: Ana amfani da igiya wajen haɗa masaƙa domin sai da ita ake iya harhaɗa bakunan kayan masaƙa.
d) <u>Dutse</u>: Ana amfani da dutse wajen haɗa jakin masaƙa. Jakin masaƙa shi ne dustin da ake ɗaura wa zare a ja shi zuwa gaban masaƙa da kuma wanda ake ɗaura wa a saman masaƙa don jan zare da shi.
e) <u>Gululu</u>: Gululu yana ɗaya daga cikin kayan da masaƙa ke amfani da shi wajen tariyar zare don samun sauƙin sarrafa zare wajen gudanar da saƙa.
f) <u>Koshiya</u>: Koshiya da ita ne ake jefa zare a tsakanin zarurukan da aka shimfiɗa don samar da tsarin da ake so na saƙa. a jikin koshiya ne ake naɗa zaren da ake, waɗanda shi tsakanin zarurukan saƙa.
g) <u>Allura</u>: Ana saka allura a cikin koshiya don a saka zarurukan da ake saka da su.
h) <u>Kunkuru</u>: A jikin kunkuru ne ake ɗaura waɗari don a samu sauƙin jawo zaren da ake saƙa da shi, shi dai kunkuru ana haɗa shi da jakin saƙa ne, waton dutsen da ake ɗaura kunkuru a jikinsa.
i) <u>Mataki</u>: Wannan mataki na saƙa, ya bambanta da na kaɗi, domin matakin a kan sa ne ake kaɗa mazari kuma da fata ake yin sa. Amma na saƙa, masaƙa ke ɗora ƙafarsu a kan sa suna shura shi a lokacin da suek gudanar da saƙa. da itace ne ake yin sa.
j) <u>Allera</u>: Allera wani ƙarfe ne da ake amfani da shi don tsayawa daga saƙa da kuma tashi da yin saƙa, wato cigaba da saƙa.

k) **Matsefi**: Matsefi wani ɗan ƙarfe ne da masaƙa kan yi amfani da shi wajen gyara tsarin saƙa, ta hanyar tsafe zaren da yake son sarƙewa a lokacin da ake saƙa.

**9) RINI**

Rini na ɗaya daga cikin tsofaffin sana'o'in gargajiya na Hausawa. Rini na tafiya ne tare da sana'o'in kaɗi, saƙa da kuma ɗinki. Saboda su ne suka samar da kayan da ake iya gudanar da sana'ar rini.

Masana sun bayyana rini da cewa:

> "Sana'a ce ta marina ke mayar da tufa irin launin da mai ita ke so".

Garba (1991:55) da Kafin Hausa da wasu (1987:55) cewa suka yi:

> "Rini sana'a ce ta sauya wa tufafi launinsu na asali zuwa wani launi da mai su yake aikata don burge sauran jama'a a wajen ƙawa ko ado."

**KAYAN AIKIN RINI**

A taƙaice dai ana iya cewa, Rini sana'a ce ta juya launi daga wata kala zuwa wata gwargwadon buƙatun mutane.

Lokacin da za a gudanar da rini, dole ne a tanadi kayan aiki da za a yi amfani da su, don su bayar da irin launin da ake so. Su ne:

a) **Baba**: Ana amfani da baba don samar da haske da walƙiya a jikin tufan da aka rina. Baba sinadari ne da ake sarrafa shi wajen haɗa kayan rini don samar da kyakkyawan launin da ake buƙata.
b) **Karofi**: Korafi dai rijiyoyi ne na harhaɗa kayan rini a cikin su don samun sauƙin saka tufafi masu yawa waɗanda ake buƙatar tura su zuwa wani launi iri ɗaya. Haka kuma rijiyoyin na iya ajiye sinadarai masu yawa kuma ya ɗauki lokaci mai tsawo ba tare da wani abu ya lalata ta ba.
c) **Toka**: Ana amfani da tokar da ake samu daga ƙananan itace da aka ƙona don gudanar da girki ko don samar da tokar saboda haɗa abubuwan rini.
d) **Maciya**: Marina na amfani da maciya wajen harhaɗa abubuwan rini da ake cakuɗa su wuri ɗaya don samar da launin da ake buƙata.

**10) ƊINKI**

Ɗinki dai shi ne aikin haɗa abubuwa musamman tufafi ta hanyar amfani da zare ko kisani da allura ko basilla.

Bello (ed) (2006:125) cewa ya yi:

> "Ɗinki shi ne sarrafa zare da allura da kyalle don samarwa jama'a sutura ingantacciya".

Wato dai ɗinki shi ne haɗa kyalle da kyale don canza kyallen zuwa wani abu daban.

Sana'ar ɗinki ta kasu gida biyu bisa ga tsarin al'adun sana'ar ɗinkin Hausawa. Farko dai akwai ɗinki don samar da tufafi ko sutura ga jama'a sai kuma ɗinki da maɗunkan huluna da ƙwaɗo da linzami ke yi. Waɗannan madunƙan suna ƙawata kayan da maɗunkan sutura suka samar.

## KAYAN AIKIN DINKI

Maɗunka kan tanadi abubuwa da zasu yi amfani da su kafin fara aikin na ɗinki, su ne kamar:

a) Sawaye: Sawaye dai wani yadi ne da masaƙa ke saƙawa don maɗunka su yi amfani da shi wajen yi wa jama'a suturar da suke so. Sawayen dai ƙwarya-ƙwarya ake sayar da su, wato maimakon a ce yadi-yadi sai a ce ƙwarya-ƙwarya.

b) Zare da Allura: Zare da allura da su ne ake amfnai wajen haɗa ƙwarya-ƙwarya sawaye don samar wa jama'a sutura da zasu yi amfani da ita.

## 11) KULI-KULI

Sana'ar ƙuli-ƙuli, sana'a ce da ake sarrafa gyaɗa don gudanar da ita. Masana sun baɗa ma'anar ƙuli-ƙuli shi ne:

> "Kuli-ƙuli shi ne tunkuzar gyaɗa da ake dunƙulawa toya da mai". Sunansa kuli-kuli ya samo asali ne daga kalmar ƙulli domin a da kulle shi ake yi a jaka ana sayarwa. Akan kira shi da sunaye daban-daban kamar haka: Bakuru, Karago, da sauransu.

## KAYAN AIKIN KULI-KULI

Akwai kayan da ake amfnai da su wajen aiwatar da sana'ar ƙuli-ƙuli, su ne kamar:

a) Gyaɗa:Gyaɗa ita ce babbar jarin gudanar da sana'ar ƙuli-ƙuli. Ita ce ake sarrafa.

b) Turmi da taɓarya: Ana amfani da turmi da taɓarya wajen motsa niƙaƙiyar gyaɗa da aka mayar da ita tunkuza don fitar da mai da ke jikinta.

c) Dutse: Ana amfani da dutse wajen matsar tunkuza.

d) Faranti Ko Faifai:Ana amfani da faranti ko faifai don ajiye mumullaliyar tunkuza don zubawa a ƙasko ko kwanon tuya.

e) Matsami: Matsami shi ne abin da ake kwashe ƙuli-ƙulin da aka suya.

f) Kwanon tuya ko Kasko: Ana amfnai da kwanon tuya ko kasko don tuya.

g) Matsani: Matsani wani kwano ne da aka huhuda shi, ya zama kamar rariya. A cikinsa ne ake zuba ƙulin da aka kwaso daga cikin mai don ya ida tsanewa.

## 12) IGIDI

Sana'ar igidi, sana'a ce inda manoma ke sayar wa mata hatsin da ba a sussuke ba (damma). Mata kan saya, su kuma su sussuke, suna sayarwa ga jama'a tsaba-tsaba gwargwadon buƙatar mai saye. Don haka sana'ar igiɗi, sana'a ce da matan Hausawa ke sayen dame ko damma ko gwallo-gwallo, su sussuke su riƙa sayarwa kwano-kwano don sauwaƙa wa talakkawa. Wannan sana'a ta igidi ta fi haɓaka lokacin kaka zuwa tsakiyar rani.

## KAYAN AIKIN IGIDI

Kayayyakin da masu sana'ar igidi 'yan taƙaitattu ne, su ne:

a) Damma: Damma ko damin hatsi ko dawa, su ne jarin masu sana'ar igidi.

b) Turmi da taɓarya: Masu sana'ar igidi na amfani da turmi da taɓarya wajen sussukar abin da suka sawo wurin manoma.

c) Korai: Masu sana'ar igidi na amfani da ƙorai don shigar da abin da suka sussuka a masussuka kuma da su ne suke zuba hatsi (tsaba) don aunawa jama'a.

d) Kwanon Awo: Masu sana'ar igidi na amfani da kwanon awo ko mudu don auna tsaba da suke sayarwa ga jama'a. kuma don daidaita mizanin kuɗin masu saye.

## 13) FAWA

Sana'ar fawa, sana'a ce da ake amfani da dabbobi ta hanyar yanka su tare a gyara namansu ta hanyar cire fatun jikinsu da tsaftace naman da nufin saida shi ga jama'a don samun abin biyan buƙata.

Masu sana'ar fawa ana kiransa mahauta. Saboda kasancewar wannan sana'a ta fawa babbar sana'a tana da ɓangarori mabambanta a cikin ta domin tana da nau'o'in gudanar da ita.

Haka ana iya cewa wannan sana'a ta fawa tana da rukononin mahauta waɗanda yanayin aiwatar da sana'ar ya samar masu. Ana iya samun mahauta da fiɗa ce kawai aikinsu kuma mafi yawan lokutta su suke sayen fatu don su sayar wa majema. Wasu kuma nama ɗanye suke saye da sayarwa. Wasu kuma suna dafawa ne ko su soya ko su gasa don su sayar wa jama'a masu buƙata don su ci.

Akwai mahauta da ke sayen ƙasusuwan dabbobin da aka yanka don su sayar wa baƙin haure ko ƙabilu.

## KAYAN AIKIN FAWA

Al'ummar Hausawa, jama'a ne masu yawa da suka fito daga ɓangaori daban-daban. Don haka ba abin mamaki ba ne a sami ɗan saɓanin wasu kayan aiki ga wani ɓangare amma kuma duk da haka mashahurai daga cikinsu da mahauta suka fi amfani da su wajen sana'arsu, su ne:

a) **Dabbobi:** Sana'ar fawa ba ta wanzuwa dole sai an sami dabbar da za a sarrafa don gudanar da ita. Mahauta na amfani da dabbobi kamar awakai, da tumaki da shanu da raƙuma da sauransu don sarrafa su wajen gudanar da sana'arsu.

b) **Igiya:** Mahauta na amfani da igiya wajen kamo dabbar da suka saya ko wadda zasu kai mahauta wurin yankawa. Sa'annan suna amfani da igiya wajen ɗaure dabbar da zasu yanka haka ma da wajen rataye dabbar da aka feɗe.

c) **Wuƙa:** Wuƙa tana da muhimmanci ƙwarai da gaske wajen aiwatar da sana'ar fawa. Duk kusan abin da za a yi cikin sana'ar fawa da wuƙa ne ake wanzar da shi. Mahauta na da wuƙa nau'i uku, akwai "balati" mai kaifi ɗaya wadda ake yankar dabbobi da ita. Haka ma ana iya gudanar da fiddar dabbar da aka yanka. Akwai kuma "barho" mai kaifi ɗaya, da ita ne ake yanka naman dabbar da aka yanka zuwa gunduwowi. Har wa yau akwai "barho" mai kaifi biyu, wannan da ita aka yanka nama don sayar wa jama'a ko al'umma.

d) **Jantaɗi:** Jantaɗi dai wani ƙarfe ne da mahauta ke amfani da shi wajen wasa wuƙarsu. Wannan ƙarfe yana da ɗan tsawo kuma mulmullale ne, sa'annan kuma akwai mai ɗan faɗi.

e) **Kurada:** Kurada dai gatari ne da mahauta ke amfani da shi wajen dandatse ƙasusuwan dabbobi da suka yanka.

f) **Itace (Gungume):** Mahauta na amfani da itace ko gungume wajen gyara ƙashin dabbar da aka yanka ko dai a gutsutture shi ta yadda za a iya sarrafa shi wajen dahuwar abinci ko kuma don a fittar da ɓargo daga cikinsu.

g) Yizga: Yizga ita ce ƙarshen bindin saniya ko sa da mahauta kan yanke su, sai a sa itace don samun abin riƙewa. Amfaninsa, shi ne suke kore wa naman ƙuda.
h) Tuguha: Tuguha ko tukufa murhu ne da mahauta ‘yan balangu da ‘yan tsire ke amfani da shi wajen gasa nama. Ana gina shi ne da ƙasa, ya yi ɗan tudu, sai a cike tudu da turɓaya. A saman sa ne ake haɗa wuta a jera tsire ya kewaye wutar har ya gasu. Amma shi balangu ana ɗora waya, wuta na garwashi har ya gasu.
i) Tunkuza/Labu: Tunkuza gumbar gyaɗa ce da mahauta masu kilishi ke sarrafa ta wajen haɗin kilishi. Haka suna amfani da ita ne wajen tsoma busasshen naman da suka tanada don yin kilishi. Sa’annan su shanya shi ya bushe kafin su gasa shi ya zama kilishi.
j) Ƙuli-Ƙuli: Mahauta ‘yan tsire ne suke amfani da ƙuli-ƙuli ne don ya ƙara wa naman armashi.
k) Yaji: Yaji shi kayan da ake haɗawa ne don yin amfnai da shi wajen sayar da nama. Kayayyaki da ake haɗa yaji da su, sun haɗa da “barkono, da gishiri da citta da masoro da ƙannifari”, wani lokaci dai “ƙuli da tafarnuwa”. Sai a haɗe su a dake wuri ɗaya a riƙa barbaɗawa masu sayen dafaffen nama ko gasasshe.
l) Takarda: Mahauta na amfani da takarda wajen ƙunshewa waɗanda suka sayi nama da ita.
m) Kwano: Mahauta na amfani da kwano wajen ɗaukar nama daga mahauta zuwa wurin sayarwa. Sa’annan suna amfani da ‘yan farantai wajen yanke gasasshen nama ga waɗanda suka saya.
n) Mahauta/Kwata: Mahauta ko kwata shi ne wurin da mahauta ke yanka dabbar da suke aiwatar da sana’ar fawa da ita. Mahauta tana da matuƙar muhimmanci ga sana’ar fawa.

## AMFANIN SANA’A GA AL’UMMAR HAUSAWA

Amfanin sana’a ga al’umma na da matuƙar yawa, amma zamu zaƙulu kaɗan daga cikin amfanin da ake samu ta fuskar sana’a. Hausawa kan ce “ƙafa ba ta tsayi inda babu ƙasa”. Wannan na nufi kowace rayuwa ba ta gudana ba tare da dogaro da wata sana’a ba. Idan aka dubi tarihin samuwar sana’o’in Hausawa za a ga cewa buƙatoci suka haifar da su. Misali buƙatar abinci ne ta haifar da farauta da noma. Haka kuma buƙatar kayan aiki na haifar da ƙira da sassaƙa. Buƙatar sutura ta haifar da sana’ar jima, da kaɗi, da ɗinki, da saƙa, kamar yadda buƙatar muhalli ta haifar da sana’ar jinka da gini. Haka dai abubuwa ke faɗaɗa bukatoci ke faɗaɗa har aka haifar da sana’o’i a fuskoki daban-daban. Abubuwan hawa sun yawaita, sai aka sami kanikawa da masu walda da masu faci a matsayin watsu sana’o’i masu zaman kansu. Idan aka dubi yanayin muhalli irin na zamani. Shi ne ya haddasa samuwar burkila, kafinta, fulanta da masu bulo. Da wannan ana iya cewa ta hanyar sana’a al’umma kan sami cigaban rayuwarsu ta yau da kullum.

A taƙaice dai sana’a ita ce madogara wajen tafiyar da rayuwar al’umma ta yau da kullum.

## KAMMALAWA

Wannan muƙalar ta yi tsokaci ne a kan fasahar Bahaushe ta fuskar sana’o’insa na gargajiya, an dubi ma’anar sana’a musamma ta la’akari da ra’ayoyin masana, da taƙaitaccen tarihin samuwar sana’o’i ga al’ummar Hausawa da kuma rabe-raben sana’o’in ta fuskar jinsi.

Haka kuma an yi nazarin wasu sana’o’in musamman ta fuskar kayan aikin da ake aiwatar da su. Sana’o’in da aka duba sun haɗa da noma, kira, kaɗi, wanzanci, sassaka, jima

da fawa da makamantansu. Daga ƙarshe kuma muƙalar ta tusgo da wasu daga cikin amfanin sana'a ga al'umma.

## MANAZARTA


Auta, Algaita, volume IV Kano: Jami'ar Bayero.

Bashir, L. (1989). Sana'o'in Hausawa: Sana'ar Koli da ta awo a Sakkwato, Jami'ar Usman Ɗanfodiyo.

Bello, S. (2006). Kamusun Hausa Jami'ar Bayero Kano.

Garba, C. Y. (1991). Sana'o'in Gargajiya a Kasar Hausa, Ibadan: Spoectrum Books Ltd.

Habib, A., Usman I. M., Rabi'u M. Z. (1982). Zaman Hausawa.

Kundin Digiri na Biyu Sakkwato, Jami'ar Usman Ɗanfodiyo.

Maidabo, M. H. (1979). Ciniki da Sana'o'i a Kasar Hausa, Thomas Nelson Nigeria Limited.

Sanyinnawal, S. I. (2015). Jirwayen Sana'o'in Gagajiya a Adabin Bakan Bahaushe,

Sharifai, B. (1990). Take da Kirarin Sanaa'o'in Hausawa na Gargajiya; Nazarin Ma'anarsu da Muhimmancinsu ga Rayuwar Hausawa. Kundin Digiri na Biyu Kano, Jami'ar Bayero.

Wushishi, S. S. (2011). Dangantakar Magani da wasu Sana'o'in Gargajiya na Hausawa. Kundin Digiri na Biyu, Sakkwato, Jami'ar Usman Ɗanfodiyo.